Wata irin ajiyar zuciya ta sauke! kafin ta dan girgiza kai, saboda gudun bacin ransa zata shiga a ganinta ai shi ya kamata ace yazo gurinta, amma Asp yafi karfin alfarma a gurinta.

Tana shiga ya mayar da kofar ya rufe.....Ta tsaya bakin kofar falon tana bin ko'ina da kallo, shuru kamar baya ciki ko'ina tsaf-tsaf! kamshi mai dadi sai tashi yake.

Ta jima a tsaye a bakin kofar falon tana sa'kawa da kwancewa kafin ta yanke shawarar da zuciyarta take ba ta.

Tana kokarin bude kofar domin fita, gyaran muryarsa ya dakatar da ita.

Kasa juyowa tayi ballanatana taga halin da yake ciki.

Asp din ne ya kira shi a waya yace ya fito falo ga amaryarsa ya kawo masa, beyi kasa a gwiwa ba ya fito sai kuma ya hange ta ita kadai tana kokarin fita.

Murmushi kawai yay yanzu ya fahimci manufar abokin nashi.

Kai tsaye gurin da take ya nufa, yana isa yasa hannunsa a kafad'arta.

Gabanta ya fadi tare da tashin tsigar jiki, wani irin rawa jikinta ya shiga yi.

Ya d'an juyo da ita domin su fuskanci juna.

Sosai tayi namijin kokarin kallonshi.....wanda har yanzu babu riga a jikinsa sai dogon wandon uniform na
d'in shi.
Rintse ido tayi gabanta na cigaba da fad'uwa, rayuwarsu a daji ce ta fad'o mata a rai.

Hannunshi ya d'auke daga kan fad'arta ya lalubi hannunta guda ya rike a nashi, Cikin taushin murya yace." Amaryata."

Gwiwarta ta dinga rawa bata tsammanci haka daga gurinshi ba, ta dauka za su cigaba da rigima kamar yanda suka saba a waya sai kuma taga akasin haka, koda yake a cikin maganganun Asp ya sheda mata cewa abokin nasa zai gyara kuskuransa.

Zuciyarta ce tai rauni! ta kasa hasala komai tana kallo ya ja hannunta har cikin dakinshi ya zaunar da ita gefan gado.....Kafin yace." Abokina yace dani wai ya kawo min ke domin kiyi min tausa! ki kuma hada min ruwan wanka ni nace kam *wane mutum!* ai idan tausar ce ni ya cancanta nayi miki a matsayinki na gimbiya kuma amarya ko ba haka bane."

Kallonshi tayi tana mamakinsa, kamar bashi ne wannan masifaffan ba mai ba'kar maganar tsiya.

Kafin ta ankara taji saukar hannunshi saman bakinta, tayi saurin kawar da kanta, bata yarda ta sake kallonshi ba, abun nasa kamar yana kokarin wuce gona da iri.

Ganin yanda tayi rauni da yawa! yasa ya rabu da ita ya shige toilet din ya bar ta da mugun

mamakinsa.

Tana nan zaune ya fito daure da babban towel a jikinsa da wani karami a hannunsa yana goge kanshi.

Ido suka had'a kawai ya sakar mata murmushi wanda yay masa bala'in kyau. dimples a kumatunsa sai kace mace.....*"GIMBIYA TA.* Ta ji wani iri a tare da ita, tana bala'in jin dadin ya kira ta da wannan sunan kamar a bakinsa aka kirkira.

Kusa da ita ya zauna da man shafawa a hannunsa.....Saurin janyewa tayi saboda kusancin nasu yayi tsanani har yanzu mamakin al'amarin take mutum sai kace aljani, koda yake dama dasu yake tu'ammali.

Da wayo da wayo sai da ya sake nani'karta ya mika mata man shafawar da fadin." Ki sha min a baya na duk da na san nayi tsaurin ido amma ina neman alfarma."

Ta kalleshi a karo na farko da tayi magana tun bayan shigowarta....."Da can waye yake shafa maka, nima da kaina nake shafa abina don haka kai ma sai kayi dubara ka shafa abunka."

Ya sake kusantar jikinta sosai yace." Ni nake shafa abina yanzu ganinki a zaune a kusa dani yasa nake miki sha'awar samun lada daga yau duk wani hidima da zakiyi min Allah zai baki lada mai yawa kuma zan d'aga miki 'kafa ki shiga aljanna da ikon Allah."

Gabadaya ya gama kashe mata jikinta, ta dinga kallonsa tana tunanin wasu abubuwa a kanshi.

Man shafawar ya mi'ka mata da ido yay mata nuni.

A sanyaye ta kar'ba ta lakato a hannunta tana mutsikawa, ta rasa ma yanda tayi ta kai hannu jikinsa, sai mutsika man take a tafin hannunta.

Hannunta ya kama ya dora a kan cinyarsa da fadin." Tunda ba zaki iya shafa min a baya na ba, shafa min anan."

Da sauri ta cire hannunta tana galla masa harara!
Zumbura baki tayi da fadin." Ni wallahi ka takura min, abinda banyi niyya ba."

Yace." Ba kya san shiga aljanna madawwamiya ko."?

Shiru tai tana cigaba da mutsika man a hannunta duk ta zama wata iri sakamakon abinda yake tsiro dashi, banbarakawai!

Ganin taki tayi abinda yake so yasa ya kyaleta yana nazari da tunanin hanya ta biyu da zai bullo mata.

Tsaf ya shafe jikinsa da mai dama neman fitina ne kamar yanda ta fada da can waye yake shafa masa.

Ba ta sake kallonsa ba har ya gama shiryawa yana fesa turare, kira ya shigo wayarsa.

Ya dauki wayar yana dubawa.

Gefan da take zaune ya kalla akayi katari suka had'a ido! bece komai ba ya janye idonsa tare dasa wayar a kunnashi.

"Hamra'u ke za'ayi wa bangajiya ai na samu sashena tsaf yana kamshi mai dadi na kuma ga daining cike da abinci iri-iri sannu kokari nagode sosai." da wannan maganar ya fara.

Jin ya ambaci sunan yarinyar yasa tai saurin kallonshi, wayarsa yake hankalinsa kwance ga wani murmushi na mussaman a fuskarsa.

Mugun haushinsa ya turnuketa shin wai me yake nufi ne.?

"Bana bukatar komai Hamra'u hutu kawai nake bukata kuyi hakuri da safe zan shigo mu gaisa sosai gaisuwata dake ta mussaman ce."

Daga daya bangaran tace."Shikkenan Yaya na, amma zan so nayi tozali da kyakykyawar fuskarka dawowarka ta sanya ni farin ciki da wuya yau na iya rintsawa."

Farin ciki ya cika masa zuciya, a rayuwarsa yana masifar son kulawa da soyayya da kuma iya kalami ta inda yarinyar ta siye zuciyarsa kenan.

Yana 'yar dariya yace."Ki kwanta kiyi barci zan zo miki a mafarki kar ki damu akwai amana a tsakanin mu."

Be ji amsarta sakamakon jin bugun kofa kafin yai aune har ta fita, da sauri ya cimmata tana kokarin bude kofar falon ta fita.

Hannunta ya rike tare da zuba mata idonsa yace." Ina zaki je kuma."?

Sosai ta daure tayi jarumtar danne masifaffen kishin da yake taso mata....."Sakar min hannu bana san damuwa zanje na kwanta dare yayi."

Ya girgiza kanshi da fadin." Asp ba haka yace ba, cewa yay ki kwana anan kuma ya sheda min cewa ka da nayi miki da k'arfi ma'ana na bi komai sannu a hankali."

Sai ta rasa inda maganarsa ta dosa....."Kada nayi miki da karfi na bi komai sannu a hankali. sai yanzu ta fahimci abunda yake nufi.....Kallon banza tai masa kafin ta fizge tana jan tsaki! bude kofa take kokarin yi ya janyo ta da 'karfi! rumgumeta yay tsam a jikinsa tare da dora hannuwansa kan mazaunanta ya riketa da kyau!

Ita dashi wani irin numfashi suka sauke sakamakon had'uwar jikinsu, gabadaya sai suka kama kyarma (rawar dari) kamar masu jin sanyi, ya wani 'kam'kamta a jikinsa yana sassana kamshin dake fita a jikin gashin kanta.

Duk kokarin da tayi gurin ganin ta rabu da jikinsa abun ya gagara domin da kyau ya rik'eta! kafafunta suka dinga rawa! sam ba tayi tsammanin wani al'amari makamancin wannan za ta faru a tsakaninta dashi ba.

Kalaman b'oyayyan masoyinta ne suka fara dawo mata a kunne....."My love ki rike min amana kada ki bari wani abu ya shiga tsakaninki dashi, baya sonki ni nake miki sasihin so ba zan bari ki wulakanta ba."

Tuna wannan yasa taji wani karfi yazo mata, tabbas da akwai dalilin da yasa yake so ya raba da budurcinta idan ba haka ba me yasa da ganin sarkin fawa sai miya tayi zaqi, gashinan a gabanta yana waya da yarinyar da yake so."

Tsananin sha'awar da ta taso masa ita ta sanyaya kuzurin sa, dalilin kenan data samu nasarar kwace kanta a hannunshi.

Ta kalleshi cikin 'bacin rai tace." Wato abunda kake nufi kenan! kana rawar jiki zaka more ko? to ba zaka samu abunda kake so ba a tare da ni domin duk na fahimci in da ka nufa, kaje ka sauya wata dubarar domin na fahimci wannan."

Cikin zafin nama ta kama hanyar fita bayan ta gama maganarta.

Kafin ta fitan ya ritsa ta.....danneta yayi sosai a jikin bango(garu) ya zuba mata jajayen idanuwansa da suke cike da tsananin sha'awa, shi kansa ba a son ransa yake aikata abinda yake ba, duk cewa yarinyar halalinsa ce amma ba yanzu ya shirya kusantarta ba.

Mayataccen kallo yake mata irin na kurrula wanda ya kassara mata duk wata gaba ta jikinta, ita

bata ta'ba ganin mayata irin ta yau ba, shin wai me yake shirin faruwa ne.?

Hannu yasa ya tallafo fuskarta ya tsirawa bakin ido!

Gabanta ya dinga bugawa! ganin yana kusanto da fuskarta kusa da tata.

Kokarin kawar da kanta take ya rike fuskar da kyau! duk dubarar ta, sai da ya samu nasarar had'a bakinsa da nata.....Harshenta kawai ya cafka ya fara tsotsarsa kamar wanda ya samu alawa.

Shi yake jin dadin kiss din amma ita kuwa gabadaya bakinta da harshenta rikicewa yay da wani irin zafi na rashin sabo.

Wani irin dadi yake ji sakamakon tsotsar bakinta, duk ya shanye mata yawun bakinta dole haka ta hakura ta dinga kar'bar nasa yawun tana shanyewa amma ba dan ranta yaso ba sai dan ba yanda za tayi.

Sosai ya galabaitar da ita kafin ya cire bakinsa daga nata.

Kuka ne ya kufce mata kawai sai ta shiga rerawa kamar ta dora hannu aka tayi ta kurma ihu!!

Hannunta ya riko, ya fara janta domin shiga daki. ta turje tana komawa baya tare da rike lalube, sosai take kuka hawaye duk ya jik'a mata fuska, mutukar ta yarda ta bishi dakinsa zai samu nasara a kanta, shine dalilin da yasa take turjewa, da fadin. "Wai meye hakane ka sakar min hannu na tafi guri na wannan ai wulakanci ne na gaji da abinda kake min."

Kansa ya shiga girgiza mata alamun ba zai yi abinda take so ba.

Tace." Wallahi ba za ka samu abunda kake so ba dan iska kawai."

Kalmar tai masa ciwo amma sai ya danne domin tafadi wacce ta fita muni a kansa. lallai yau zai nuna mata kalar iskancinsa.

Ta dinga dukan hannunsa tana komawa baya kawai sai ya sa'bata a kafad'a! ya tallafe mazaunanta, kai tsaye dakinsa ya nufa da ita sai duka da cizo da yakushi take masa amma ko gezau! wata irin power da fitina yake ji.

Saman gado ya jefar da ita ya tsaya a kanta da fadin." Kin jima kina zagina tare da kira na da kalmomin 'batan ci, iskanci ba hali na bane amma yau zan gwada miki shi."

Hanyar fita ya nufa ta bishi da wani irin kallo na fargaba da tashin hankali, tana jin sanda yake murzawa kofar key daga waje, taji kamar tace wayyo Allah ta shiga uku. wace irin masifa ce wannan ace mutum daga dawowarsa ko hutawa beyi ba zai fara wani abu, gaskiya tayi mamakin hakan kuma ba tayi tunanin faruwar hakan da wuri ba, koda yake wani irin shaid'anin mutum Allah ya had'ata dashi wanda duk tsanani ba'a iya gane kansa

"Kada ki kuskura ki yarda dashi akwai manufarsa a kanki."

Zuciyarta ce take bata wannan shawarar, wanda ita ma a karan kanta tunanin da take kenan, idan babu wata manufa tana ganin ba zai saurareta ba idan anyi duba da irin rashin arzikin data dinga tafka masa watakila yana so ya fanshe ne ta wannan sigar.

Ta shiga rud'ani sosai! da tunanin mafita, duk wayo da dubarar ta, sun 'kare me za tayi a yanzu domin kare kanta bayan ga ta zaune a saman gadonsa sai kuma yanda yayi da ita tunda ya fita 'karfin ta mugunta zai gwada mata.....Hawaye masu zafi suka 'kwace mata anya kuwa? ba zata ta'ba yarda ya samu nasara ba.

Kika futar min da littafi keda Allah! ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!

#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE
[2/11, 2:32 PM] Matar Malam: *LOVE💔*

 GSUR
65&66
Duk cikin tarin abincin da aka shirya masa na tar'ba guda d'aya ya iya ci, towon alkama da miyar ku'bewa wannan shine favorite d'inshi tun yana yaro yana san towo mussaman na hatsi, na shinkafa ne bai fiye ci ba shi din ma yana ci amma ba sosai, da tissue ya goge bakinsa, kafin yayi godiya ga Allah ya dauki wayarsa dake saman daninig yana d:an dubawa.....WhatsApp ya shiga ya duba number ta ba ta jima da sauka ba. sako ya tura mata a matsayinsa na b'oyayyan masoyinta.

"Assalamu alaikum."
"My love yau ina cikin b'akin ciki a sakamakon dawowar mijinki, jikina kawai yake bani kamar wani abu zai shiga tsakaninku my love don Allah kada ki manta alkawarin mu, ki rike min amanar kanki
FARUK mijinki da ikon Allah."

Yana tura mata messenge din ya kashe wayar ya mike, kai tsaye dakin ya nufa da tunanin wani

abu a cikin ranshi.
Shi kansa baya son aikata abun amma shine target d'inshi a kan yarinyar.

Motsin bud'e kofar ne ya zaburar da ita, gabanta na bugawa ta zubawa kofar ido ya shigo da sallama a bakinsa, bata iya amsawa ba sai dai uban kallon da take masa.

Ya juyo suka hada ido nan ya hango tsoro da firgici a tare da ita.

Sake tamke fuska yayi kamar bashi ba, rigar jikinsa ya fara kokarin cirewa tayi saurin kawar da kanta, tun ba yanzu ba take jin shakkun kallon zahirin sa, yanayin girman kirjinsa da yanda gashi yake kwance ba'ki'kirin yana masifar jefa ta a damuwa, tun zamansu a daji ta fahimci hakan.

Fitilar dakin ya kashe , tana ganin haka sai ta sakko daga bed din ta samu bango ta jingina kafafunta na wani irin rawa!.

Ya gan ta sai ya nuna kamar bai ganta ba, yazo yana lalube a gadon da fadin." Kina ina ne ga d'an iska yazo iskanci."

Tayi saurin nufar k'ofar fita don duk a tunaninta ya bar kofar a bude, taja taji a rufe gam! hawayen da take dannewa suka kufce zuba kawai suke a saman fuskarta, ita kam bata shirya wani lamari yanzu ba sai taga kamun ludayin zamanta dashi.

Ya kunna wayarsa yana haske ta, ya hangota rungume da kofa sai sheshsheka takeyi jikinsa ya bashi kuka take duk da tana kokarin boyewa. ko da alama bata bashi tausayi ba, beyi niyyar yi mata komai ba kalmar data kira shi da ita itace ta sauya masa ra'ayi.

Da asalin muryarsa yayi mata magana.

"Ki zo kawai domin wahalar da kanki ki ke na rufe kofar kuma mai kwatarki a hannuna sai wanda ya shirya."

Shuru tai ba tace komai ba kuma bata motsa daga gurin da take ba.

Nufar idan take yayi, sai kawai saukar hannunsa taji a kafadarta, ta goce sa sauri ta sauya guri.

Da lalube ya lalubo ta ya rike tsintsiyar hannunta da kyau! janyota yayi da karfi ta fadi a jikinsa, yasa hannu ya rike ta suka nufi gadon, suna tafiya tana dukan kirjinsa da fadin "Ka sake ni wai dole ne sai ka cutar dani? bana sonka domin ban shirya zama da kai ba ballanatana na amince da bukatarka."

Shuru kawai yay mata domin duk wannan surutan da take ba zasu ha nashi abinda yayi niyya ba.

Yana zaunar da ita ta zabura! za ta tashi tsaye ya tura da hannunshi ta fadi saman gadon.

Kirjinta ya danne da hannunsa guda yasa kafafunsa ya take nata, sai kokarin kwatar kanta take ta kasa.

Ba kyaleta ba sai da ya tabbatar ta daina buge-bugen da take sannan ya kwanta kusa da ita yana mayar da numfashi itama numfashin take saukewa.

Gefe can ta matsa ta hade jikinta guri daya tana sauke ajiyar zuciya jikinta duk yayi tsami! Asp ya ha'ince ta domun ta tasan abinda zai faru kenan da bata yarda da uzurinsa ba.

Hucin numfashinta taji a kusa da ita, rintse idonta kawai tayi tana jiran abinda zai faru! aikuwa bakinsa yasa a wuyanta ya dinga sumbata yana sakin wani irin nishi!

Shuru tai kawai tana jin abinda yake, addua take Allah yasa ya tsaya a haka.

Adduarta bata kar'bu ba domin ji tay yana kokarin cire mata alkyabba, da sauri ta rike igiyar gam! a hannunta!

Birkito da ita yay suka kalli juna, k'wayar idonshi kawai ta iya gani saboda duhun dakin, jin yanda numfashinsa yake sauka a fuskarta yasa ta kawar da fuskarta.

Hannuta ya cire ta sake mayarwa gurin ta rike da kyau.

Kawai sai ya haye kanta ya raba kafafunsa amma be sakar mata nauyinsa.....Cikin wani irin voice yace." Kada mu wahalar da junanmu domin abinda nayi kudiri ba zan fasa ba.

Ta numfasha kafin tace." Nima ba zan bari ka mori wani abu nawa ba domin baka cancanta ba."

Yace." Waye ya cancanta.'?

Shuru tayi tana kawar da kanta.

Yace." Kinyi shuru ki fada min wanda ya cancanta da ya mori wani abu naki."?

Duk da tana jin tsoron furta maganar.....Tace." Ina nufin masoyina na gaskiya wanda

kaunarsa take dan'kare a raina, shine wanda ya cancanta da nayi rayuwar jin dadi dashi.

Murmushi yayi kafin yace."Dake masoyin naki duk baku da hankali! okey yanzu dai tunda kinqi yarda muyi cikin kwanciyar hankali, zan gwada miki karfina."

Yana gama maganar ya hade hannunta ya rike da hannu daya, kafin ya fara kokarin raba ta da kayan jikinta.

Dukansa take da kafafunta amma ko gezau! yau so yake ga iyakar gudun ruwanta.

Haihuwar uwarta yayi mata don ko arzikin wando bai barta dashi ba ballantana abar banza breziyya.

Ta ture kirjinsa tana kokarin tashi yasa hannunsa a kirjinta domin mayar da ita, hannun nasa ne ya sauka kan dukiyar fulaninta, yaji wani shocking a jikinsa, be yarda ya cire hannun ba kawai ya zarce da wasa da breast din yana jan wani irin nishi, jikinta wani irin taushi da k'amshi ga breast dinta ya cika masa hannunwa yana jin dadin wasa dasu ya dinga jan nipples din yana so yasa a bakinsa amma yana tunanin wani abu.

Wani irin yanayi ta shiga sakamakon abinda yake mata, gabadaya sha'awarta tashi! lokaci guda ta rikice ta dinga motsi tana had'e jikinta ruwan ni'ima kawai yake fita, shashsheka take tayi tana sake sakin jikinta a gadon, duk ta daina kokarin da take na kubtar da kanta, yanda yake wasa da breast dinta ya dauki hankalinta, ta dinga lumshe ido tana ciccije bakinta.
Tuzuru! da Tuzuruwa! dama abinda zai faru kenan🤠

Shima karkarwar kawai yake, kokari yake ya tsare kanshi kada ya aikata wani abu yanzu amma tsabar yanda jijiyarsa take harbawa yasa ya kasa sarrafa kanshi, jiki na mazari ya cire komai na jikinsa ya manneta a jikinsa fatarsu ta had'u! zazzafar ajiyar zuciya suka dinga saukewa a tare suna malelekuwa a gadon, gasu 'kankame da juna hatta da yatsun hannuwansu a had'e suke.....Suna jima haka kafin ya dan cire kanshi yana laluban fuskarta, bakinta yake nema.

Ba ta iya hana shi ba, to ina kuzarin ma da zata bijire masa, ai da zasu dawwama a haka tana so domin jin ta take kamar mai yawo a gajimare.

Kissing dinta yake personality yana cigaba da wasa da hannuwansa a sassan jikinta.

Motsin kawai take tana neman d'auki domin wani irin rawa gabanta keyi wani abu yake mata irin wanda be ta'ba yi ba.

Yanayin abinda takeyi yasa ya fahimci abinda yake da akwai, hannunsa ya kai gurin, ta zabura! tana sakin wani irin nishi.....Shi kam jin gurin jike da lema yasa jikinsa mutuwa, yaji gabadaya ya kwad'aita da shiga 'koramar, shin wace irin ni'ima ce wannan da take bin hannunsa, ko dai

ta samu satisfaction ne? cikin zuciyarsa yake wannan tunanin.

Sam ba taso ya cire hannunsa a gurin ba, taso ya cigaba da abinda ya fara ta dinga sauke ajiyar zuciyar zuciya tana shashshafa jikinsa wanda bata san ma ta nayi ba.

Cire bakinsa yay daga nata ya mayar kirjinta ya fara shan breast din a karo na farko da faruwar al'amarin.

Hakan yay mata dadi sai dai yanda yake sucking din nipples din ya sake jefata cikin bukata domin ta gigice ta gama kaiwa ma'kurar 'kurewa! kamar ta fashe da kuka haka take ji yanayinta, mazari! kyarma! rawar jiki da wani irin gumi su kawai take, tana fitar da wani irin nishi!!! kafin ta kank'ame shi a jikinta tana sakin karamin ihu!!! wani irin relief taji gabadaya kamar an sauke mata wani mugun nauyi, yanda ta saki jiki ta daina motsi ya tabbatar masa da cewa ta samu gamsuwa, godiya yay ga Allah a zuciyarsa domin tun farkon fara al'amarin ya fahimci raggon namiji ba zai iya da ita ba, domin yanayin ta ya nuna masa cewa tana da 'karfin sha'awa beyi tsammanin wannan abun da sukayi zai gamsar da ita ba, koda yake salon da yayi mata kad'ai ya isa ya gamsar da ita ba tare da an shiga wannan gurin ba, dama bai shirya hakan a yanzu ba, yana so ya ragewa kanshi zafi shiyasa ya bullo da wannan dubarar.....Shima ya samu satisfaction amma ba irin yanda yake bukata ba, a san samu yayi nin'kaya a cikin 'koramar da yake jin zubar ruwanta a jikinsa, amma saboda wani dalili nasa ya sanya ya daure yana kuma kokarin kwantar da joystick din shi wacce take ta wani irin harbawa tana motsi da alama bata samu abunda take so ba.

Yana niyyar sauka daga jikinta ta fara tureshi tana zumbura baki tare da kawar da kanta.....Bece mata komai ba ya sauka wandonshi yasa ya suturta kanshi kafin ya kunna fitilar dake gefen gadon, dakin ya gauraye da haske.....Idonta a rufe taga alamun haske da sauri ta bude ido ta ganshi ya tsirawa jikinta ido yana kallo.....Kamar ta zabga ihu! ta fara jan bed shirt domin rufe jikinta, ya rike bedshirt din still idonsa 'kuri a kanta yarinyar nada dadi abinda yake aiyanawa kenan a ranshi.

Alkyabbar ta dake yashe a k'asan gadon tayi saurin d'aukowa ta rufe jikinta ranta gabad'aya ya gama b'aci! da abunda yake, a ganinta wannan wulakanci ne kawai zai kunna fitila domin ya kalli tsaraincinta, tun dai bukatarsa ta biya shikkenan....*🤠 Uwar iya kenan!* duk hararar da take zabga masa bai sa ya janye idonsa ba sai da ya ga dama tukkuna ya sauke ajiyar zuciya mai zafin kafin ya yunkura ya tashi ya kama hanyar toilet domin tsabtacce jikinsa.

Kallo ta bishi dashi tana ayyana abubuwa da yawa a kanshi, ta kowane bangare ya cika cif! yana kuma sawu na farko a cikin mazan da kowacce mace zata bukata ace mijinta ne, abunda yayi mata a yanzu shiyasa ta gazgata hakan, sakayau! take jin mararta babu wani damuwa, duk tarin sha'awar da take damunta lokaci gudu yay mata magani ta hanyar

romancing kad'ai! tana bala'in san irin wannan soyayyar shiyasa ta gaza ha na shi aikatawa, a ganinta hakan ba zai shafi rashin jituwarsu ba, mutukar zai dinga bata kulawa irin wannan zata amince amma ba zata yarda da ya rabata da budurcinta ba, sai ya furta mata kalmar so da bakinsa ta tabbatar da gaskiyar maganarsa, zata iya zama dashi saboda wannan dalilin.

Ya fito ya sameta tana ta sa'kawa da kwancewa, ya kalleta da fadin."Ina fatan dai Kin iya wankan tsarki ko."?

Cike da mamaki ta kalleshi wace irin magana ce wannan.....Cikin gatse tace "Ban iya ba."!

Ya girgiza kanshi da fadin." Ban yi mamaki ba." ya fada tare da kokarin barin gurin.

Kallon takaici take masa tana mamakin rainin hankalinsa, ko ya d'auka ita din jahila ce."

Tsaki mai tsayi taja tana hararar bayanshi lokacin da yake kokarin sanya jallabiya.

Sarai yaji lokacin da take tsakin amma bece mata komai ba ya lura kamar hakan dabi'arta ce. *(Yawan Tsaki ba abun arziki bane ballanatana ga miji, mata don Allah mu kiyaye kada mu bari bakinmu ya saba da jan tsaki)* Cigaba yayi da shirya jikinsa yana tunanin hanyoyin da zai bi gurin sauya mata munanan d'abi'u

Zanin les d'inta ta d'aura ta yafa dankwalin a jikinta ta nufi toilet tana jin wani irin bacin rai da damuwa a cikin ranta, abinda ya faru a tsakaninsu duk ya dameta.

Toilet din ya bita lokacin tana tsugune da ruwa a gabanta amma bata fara wankan ba.

Tsayuwarsa ya gyara har da rungume hannu a kirji ya zuba mata ido so yake ya gani shin ta iya wankan tsarkin ko bata iya ba.

Daburcewa tayi ta dan harareshi da gefen ido da fadin." Wai meye haka zaka sani a gaba kana kallona ko kuma abunda kayi ne be isheka ba."?

Be tanka mata ba har yanzu idonshi na kanta kuma bashi da niyyar fita.

Ta sauke ajiyar zuciya tsaki take so tayi amma tana jin tsoron abinda zai biyo ba, haka nan ba yanda za tayi ta fara watsa ruwa a jikinta kafin ta dauki soso da sabulu.

Ganinshi tayi a gabanta.
Ta kalleshi kamar ta kurma ihu!! shin wai wane irin takurawa ne wannan.

Ruwan dake gabanta ya zubar ya had'a wani duk tana kallonshi, ya 'bata rai da fadin." Ba kiyi

dai-dai ba bari na nuna miki."

Taji kamar ta gallawa fuskarsa mari! saboda takaici, da 'kyar tace." To dama wa aka haifa da iyawa kowa a duniya ya ko ya."

Yace." Kada kiyi min rashin kunya ranki zai 'baci yanzu."

Ta kalleshi taga yanda ya 'bata rai! dauke kanta tayi zuciyarta cike da takaici

Rigar jikinsa ya cire amma ya bar gajeran wando ya tsuguna kusa da ita da fadin." Kalle ni nan."

Saboda babu yanda za tayi yasa ta juya tana kallonshi.....Yace." Da farko za kiyi niyyar irin wankan da za kiyi a zucci ko a fili kafin ki ta'ba ruwa, ina so kiyi min niyyar wankan janaba da bakinki."

Ta zumbura baki da fadin." Wani abu mukayi gagarimi! wanda lallai sai nayi wankan tsarki."?

Ya kalleta da mamaki a tare dashi yace." Okey kin raina abinda ya shiga tsakaninmu kenan."?

Shuru tayi tana dauke kanta.

Ya girgiza kai da fadin." Akwai karanci ilimin addini a tare dake wankan janaba ya wajaba a kanki dalilin ruwan da kika fitar, ko zakiyi min musu baki fitar da komai ba."

Shuru tai ba tace komai ba.

Yace." Kinji dad'i har wani ruwa na mussaman ya fita daga jikinki a lokacin nutsuwarki ta dawo daidai wannan shine dalilin da janyo miki wanka domin tsarkake jikinki wajibi ne wannan, maziyi kadai zaki fitar ki wanke abinki kana ki cigaba da ibada da wannan kawai addini ya yarda."

Jikinta yay sanyi domin ita tayi tunanin tunda romancing kawai sukayi ba za tayi wankan tsarki ba sai da soso da sabulu.....*(Hakan yana faruwa ga ma'aurata masu 'karanci ilmin addini za suyi wassani a tsakaninsu har su gamsuwa amma kuma ba za suyi wankan tsarki ba saboda suna tunanin kamar janaba bata hau kansu ba, wannan ba dai-dai bane mutukar wani abu ya fita kuma an ji dadi an samu gamsuwa to janaba ta wajaba dole idan ana so ibadah ta cika sai an wanke wannan janabar.*

*_(Nawaitu gusulul janabati-far'kul hadasul akbari-Wal-asgari_*) Za'a karanta sai uku kafin ta'ba ruwa alwala za'a fara d'aurawa a jika kai jagab da ruwa sai an tabbatar ruwan ya ratsa ko'ina sannan sai a tashi tsaye a fara wanke b'angaran dama a zuba ruwan a ko'ina kafin a tafi b'angaran hagu nan ma haka za'ayi sai an tabbatar da cewa ko'ina ya wanku sannan.

Da kanshi yay mata wankan tsaf! besa wani abu a ransa ba ballanatana hankalinsa ya tashi! ita kuwa sai no'kewa take tana jin wani iri da nauyin sa, kawai dan yafi karfinta ne.

Tsaf ya kammala ya cire towel ya mika mata, da sauri ta kar'ba ta daura.....Karami ya dauko ya daura mata a saman gashinta da yake ta digar da ruwa. ba tace komai ba ta kama hanyar fita, jikinta duk sanyaye.....Zanin les din da dankwalin ya d'auka yabi bayanta dasu a hannunsa....

SAI ALLAH YA KAI MU MONDAY DA IKONSA🙏🏻

AYI HUTUN K'ARSHEN MAKO LAFIYA

#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE
[2/13, 9:08 PM] Matar Malam: *67&68*
D'aya daga cikin dogwayen rigunanshi ya dauko mata sabuwa ya mika mata da fadin." Kisa a jikinki kafin gari ya waye ko."
Kallonshi tayi da fadin." To ka bude min kofa kawai na tafi guri na meye amfanin kwana na a dakinka." ? Da mamaki a tare dashi yace." Kece kike ganin kamar kwanan ki anan bashi da amfani amma ni ina mai tabbatar miki da cewar kwananki a dakina zai janyo miki samun lada a gurin Allah, wannan shine abinda nake miki sha'awa.

Shuru tayi tana auna maganarsa, yanda ta fahimta kamar yana so suyi zaman lafiya ga yanayin yanda yake kawo mata 'kauli da ba'adi Allah yace Annabi yace ba da son ranta ba ta kar'bi rigar ta ajiye a gefanta, shi kuma bed din ya hau yana gyara bedshirt din daya cukurkude.

Breziyyar ta dake saman gadon ya mika mata, tayi saurin kar'ba tare da dauke kanta.

Bacci ne a idonsa saboda haka yana gama gyara shimfidar gadon ya kwanta tare da rufe jikinsa da bargo, rufe idonsa yay yana addua a cikin zuciyarsa.

Wata irin ajiyar zuciya ta sauke, jiki babu kuzari ta dauki rigar tasa a jikinta ba tare da ta mayar da breziyyar ba pant d'inta dama yana toilet anan ta cire ta ajiye saboda ya riga ya b'aci dole sai an wanke.

Can nesa dashi ta kwanta da yake blanket din mai girma ne ya ishe su rufa ba tare da wani ya takurawa dan uwansa ba.

Ya bude idonsa ya hangeta a can nesa dashi ta juya masa baya bece mata komai ba ya mayar da idonsa ya rufe yana sauke ajiyar zuciya.....Ya riga ta bacci saboda yanayin gajiyar dake tattare dashi, ta dinga jin saukar numfashisa cikin nutsuwa hakan ya sake tabbatar mata da cewa bacci mai nauyi ya daukeshi. Ajiyar zuciya ta sauke ta gyara kwanciyarta idonta ta rufe tana addua a cikin zuciyarta cikin ikon Allah itama baccin ya d'auketa.

Da asubah shi ya tashe ta bayan ya shirya zuwa massalaci, sai da ya tabbatar ta tashi tukkuna ya fita.

Tana idar da sallah, ta nemi kayanta ta mayar jikinta, ba ta jirayi dawowarsa ba ta kama hanyar sashenta.

Su Kawu Ado A massalacin suka same shi saboda haka ana idar da sallah, gabadaya sai suka nufi gidan a tare kowanne cikin walwala da farin ciki, kai tsaye sashen Uwale suka nufa domin gaisawa a tsanake.

Sai da yayi musabaha da kowannesu ya dinga tambayarsu iyalinsu da sauran 'yan uwa da basu samu damar zuwa ba, Kawu Ado yace." Kowa lafiya lau UMARU suna maka fatan alkari.

Cike da jin dadi yace." Nagode sosai Kawu amma zaku dan kwana biyu kafin ku tafi ko."

Yace." Aa yau zamu tafi saboda dukkaninmu muna da ayyuka, muna jiran rana ta fito tukkuna."

Yace." To babu laifi Kawu hakan yayi, Nagode kwarai da wannan karamacin."

Yace." Babu komai Umaru amma ina da muhimiyyar maganar da nake so mu tattauna a tsakaninmu."

Ba tare da ya Kawo komai a ranshi ba yace." To babu damuwa Kawu Allah yasa alkairi ne." Yana murmushi yace." Alkairi ne da ikon Allah."

Uwale ce ta fara fitowa daga dakin kafin sauran matan su biyo bayanta.....Ganinsa a zaune yasa farin ciki ya rufesu.

Samun guri sukayi suka zazzauna kafin a fara gaishe-gaishe.

Sosai yaji dadin ganin yan uwansa maza da mata ya dinga biyewa shirmansu yana dariya da yake a cikinsu akwai wanda wasa yake a tsakaninsu sai tsokanarsa suke yana biye musu suna dariya.

Hamra'u ce ta shirya musu abun karyawa har kala biyu, tazo ta sheda musu cewa ta kammala.Kawu Ado ya dinga sanya mata albarka da irin dawaniyyar da take dasu tun bayan saukarsu a gidan.

Shima Umar din yaji dadin hakan, domin da babu ita to tabbas za'a ji kunya idan akayi duba da irin kalar matar gidan, wanda a tunaninsa nauyin kula da 'yan uwansa yana wuyanta.

Sashensa ya nufa domin barin su suka karya a tsanake.

Dama bai tsammaci samunta a sashen ba, ya kalli agogon dake kafe a dakin tara saura na safe.....Jalliyar jikinsa ya cire ya zauna gefan gado daga shi sai gajeran wando.

Wayoyinsa dake ajiye kan bedside ya dauka duka ya kunnasu.....tarin messages da suke kan wayar ya fara dubawa, kafin yaji shigowar wani messenge din a daya wayar.

Da sauri ya dauka domin yana tsammanin message din daga gurin ta ne dalili number ta ce kawai akan wayar sai ta Asp

Aikuwa itace take bashi amsar text din sa na jiya.

" FARUK Kayi hakuri tun jiya ka turo min sako babu replay sai yanzu, kada ka samu damuwa nayi maka alkawarin kare maka kaina, kuma duk rintsi ba zan bari wani abu ya ratsa a tsakaninmu ba ni taka ce har abada."

Ya karanta text din ya kai sau biyar, yana nazari da tunanin kalamanta.....Murmushi kawai yay yana mamakin al'amarin, ba zata bari wani abu ya ratsa tsakaninsu ba, amma mai yasa jiya ta kasa sarrafa kanta sai yanda yayi da ita, aka ce wai maza sun fi iya yaudara to yau ya 'karyata wannan magana domin ga yaudara nan kiri-kiri yana gani, be yarda da soyayyar da takewa boyayyan masoyin nata ba.....Ba tare da ya bata amsa ba ya ajiye wayar, ya cigaba da duba mai muhimmancin.

A nutse ta shigo da sallama a bakinta, shuru falon, da alama yana daki, saman daninig ta ajiye kwandon abincin dake hannuna.

Tayi jim! tana dan tunani kafin ta yanke shawarar buga kofar dakin nasa.

Yana jin bugun ya tsammaci yarinyar ce, be so hakan ba, saboda yana gujewa abunda ka iya zuwa ya dawo.

Jallabiyarsa yasa kafin ya bude mata kofar.

Ya dan saki fuskarsa tare da kiran sunanta.

Farin cikin ganinsa ya cika mata zuciya, wani irin kallo tai masa kafin ta amsa da fadin." Barka da asubah Farin cikin zuciyata." Ya amsa da "Barka dai fatan kin tashi lafiya."?

Ta dan girgiza kai da fadin." Lafiya lau amma kwana nayi ina mafarkin ka." Murmushi yayi yana mata wani irin duba, kafin bakinsa ya subce gurin fadin." Nima haka da kyar na iya rintsawa saboda tunaninki."

Taji wani irin sanyin dadi a ranta, tace." Nagode sosai masoyina ga abun kari na kawo maka, sannan ina so na gyara maka dakin ka."

Yace." Okey to godiya nake my love Allah yay miki albarka."

Ta amsa da "Ameen tana kokarin shiga dakin ya bata hanya yana bin bayanta da kallo, yarinyar tausayi take bashi mutuka, ta jima tana dawainiya dashi da kakarsa babu shakka idan bai aureta ba yayi butulci, nagartaciyyar macace irin wacce take da wahalar samu, dole ya cika muradin zuciyarsa.

Tana tsaka da karkad'e bedshirt din breziyya ta fad'o kasan kafafunta.....Gabanta ne yayi mugun fad'uwa, lokaci guda kafafunta suka shiga karkarwa!

Jiki a mace ta tsirawa breziyyar ido tana tunanin wani abu.....Wato daga dawowarsa har wata mu'amula ta shiga tsakaninsu? shin ina 'kiyayyar da sukewa junansu take? wasu zafafan hawaye ne suka k'wace mata tana gogewa wasu na zubowa, wani mugun kishi ne ya dinga yun'kuro mata, ta dinga ji kamar ta dora hannu aka ta dinga zabga ihu! ko ta taji sassaucin abinda take ji a cikin ranta.

Sosai take kuka sai kace wacce uwarta ta mutu! mugun haushin gimbiyar take idan akwai wacce ta tsana a duniya to itace.

Ta gama gyara dakin cikin halin ni 'yasu kafin ta kama hanyar toilet tana had'a hanya kamar wata 'yar maye, Wai UMAR din ta masoyinta shine ya fara mu'amula da wata mace ba ita ba.

Tana shiga toilet din taci tuntunbe da pant a k'asan ties, da sauri ta janye kafarta, gabanta ne ya tsananta fad'uwa, ta jingina jikin bango(garu) idonta kuri kan pant din tana ayyanawa abubuwa da yawa a cikin ranta

Da tasan mugun ganin da za tayi kenan da ba tayi sha'awar shigowa dakin ba.

Wani nannauyen abu yazo ya tsaya mata a wuya, ganin pant da breziyya ya gama kashe karsashinta, al'amarin ya bata mamaki mutuk'a sam bata kawo cewa wani abu zai shiga tsakaninsu a kusa ba.

Kafarta tasa ta ture pant din, cikin rashin kuzari da kunar zuciya ta gyara toilet din ta fito zuciyarta dankare da kishin gimbiyar ji take kamar taje ta shake mata wuya saboda yanda take jin wani bala'in haushinta a cikin ranta.

Tana fitowa suka hada ido yana zaune a daining yana karyawa, kallonta yake yana mamakin yanda idonta yayi ja! da alamun kuka a tare da ita

Kasa had'a ido tayi dashi ba tare da tace masa komai ba ta kama hanyar fita.

Cokalin dake hannunsa ya ajiye ya kira sunanta.

Tsayawa tayi amma bata juyo ba.

Yace."Me ya sami idonki sunyi jawur! domin ba haka kika shigo."

Kamar me jiran kiris sai kawai ta fashe da kuka kariris! al'amarin ya bashi mamaki mutuka gaya! ya mike da niyyar zuwa inda take, a gaggauce ta bude kofa ta fita tana share hawaye.

Sai kawai yayi tsaye a tsakiyar falon yana mamakin al'amarin.

Da yake sun shagala da hira a tsakaninsu babu wanda ya lura da shigowarta sai Ladidi wacce ta kasance 'yar uwa Dayyiba wato mahaifiyarta.....Itace ta lura da shigowarta.

Sai kawai ta tashi ta bi bayanta dakin, ta sameta tana kuka!

Zama tayi kusa da ita tana tambayarta, sai kawai ta rungumeta cikin kuka tace." Ladidi na rasa ya zanyi da rayuwata Umaru yana wahalar da zuciyata gani nake kamar yaudarata yake tunda ya auri 'yar sarauta ba zai aureni ba.

Hannu tasa tana share mata hawaye tace." Hamra'u mu ma tunanin da muke kenan, muna ganin kamar wannan yaro wasa yake mana da hankali domin idan da wacce ya kamata ya aura kece duba da irin hallacin da ki kayi masa, amma saboda rashin adalci lokaci guda muka samu labarin auransa da 'yar sarki, da muka fito muna magana kakarsa ta goya masa baya cewa ai bashi yarinyar akayi ba a son ranshi ba ya aureta ba idan gaskiya ne al'amarin me yasa ba'a had'a auran a lokaci daya ba, kakarsa Uwale ba taso ya aureki ba domin da taso ya aureki da

tuntuni anyi angama idan ma haihuwa ce da tuni kin haihu, amma babu komai, akwai hanyoyin da zamu bi domin biyan bukatarmu domin ba zamu bar wannan daular ta wuce mu ba."

Tana sauke ajiyar zuciya tace." Ladidi wannan al'amarin dole sai an nemi taimako don ganin tabbatuwarsa ki shed'awa Inna ta duk abunda yake faruwa domin a yanzu babban burina naga na mallaki Umar a matsayin mijina uban 'ya'yana."

Tace." Kada ki damu daga zarar mun isa gida zanje na sheda mata duk abunda yake faruwa dole sai ta tashi a tsaye domin idan lamari irin wannan ya tunkari mutum ba zama zai yi ba sai ya tashi ya nemi taimako daga gurin Malamai."
 (Subahanallahi Allah kasa mufi karfin zukatanmu, Allah kada kasa mu gaza gurin neman biyan bukata a gurinka, Allah ka sanya mana imani a zuciyarmu)

Yana kokarin fitowa daga part din shi Asp ya kira shi, ya sanya wayar a kunnanshi da sallama a bakinsa, Asp ya amsa yana 'yar dariya shima dariyar yay kafin su gaisa cikin girmama juna, Yace." Ya kwanan amarya."?

Murmushi yayi tare da d'an sosa gemunsa yace." Ta nan lafiya yanzu zan shiga gurinta yanzu."

Yace ." A'a ban gane ba, kana nufin kace min ba tare kuka kwana ba"?

Yace." Tare muka kwana da asubah ta gudu."

'Yar dariya yay da fadin." Taji maza kenan shiyasa ta tsere kai kuma ai kayi gaggawa."

Dariya yay kafin yace." Kai fa kake min fada na gyara kuskurana kuma nayi mata kalamai na soyayya ta bada kai a garin hakan na kasa daurewa kawai na ragewa kaina zafi."

Cike da jin dadin faruwar al'amarin yace." Alhamdulillhi nayi farin ciki da jin hakan, wannan shine mataki na farko da zai sa ku sasanta kanku, Allah ya baku zaman lafiya da zuria dayyiba."

Ya amsa da "ameen suma ameen mutumin kirki nagode kwarai da karamci." Yace." Babu komai Umar mun riga mun zama daya da juna idan ka shiga ka mika min gaisuwa gurin amaryar." Yace." Za taji insha Allah." Sallama sukayi cikin mutunci da mutuntawa.

Kika futar min da littafi keda Allah! ki ka karanta baki biya ba kema keda Allah!

#500via.....0542382124.....Binta umar gtbabk, idan kati zaki turo kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number.... 07084653262.....BINTA UMAR ABBALE

[2/16, 3:25 PM] Matar Malam: *69&70*
Tun lokacin da Kawu Ado ya fara magana yake girgiza kai yana mamakin al'amarin, koda yake ba abin mamaki bane idan akayi duba da irin rashin tarbiyar yarinyar, zagi da cin mutumcin d'an adam abune mai sauki a gurinta, sosai ransa ya 'baci da irin tozarcin da tayi wa 'yan uwansa dama abinda yake gudu kenan, yana k'aunar family nasa gaba da baya duk talaucinsu da rashin wayewar su shi ba zai k'yamace su ba tunda sune k'ashin bayan samar dashi, sannan tare dasu yayi rayuwa saboda haka ba zai zama wani abu a duniya ya wofintar dasu ba, dole ya nuna mata muhimmancin 'yan uwansa domin a gaba ta kiyaye.

Kawu Ado ya sauke numfashi da fadin." Saboda haka Umaru mu ba zamu ce ka rabu da yarinyar nan ba, taci albarkacin mahaifinta, amma tilas ka auri wacce tasan kima da mutunci da darajar mu, ina nufin yarinyar nan Hamra'u itace wacce ya dace ka aura tun kafin zuwan wannan al'amari, saboda haka wannan ba shawara nake baka ba umarni ne a matsayina na wanda ya isa ya fada maka magana kaji, idan kuma ban isa ba to sai na cire hannuna daga kanka."

Ajiyar zuciya mai zafi ya sauke kafin yace." Kawu ka isa ka zartar da ko wane irin hukunci a kaina domin a yanzu bani da kowa sai kai sai kuma Uwale tare da sauran 'yan uwana ina alfahari daku mutuka, kuma ya zama dole na sanya kafar wando guda ga duk wanda yayi nufin tozarta ku, kamar yanda ka bani umarnin auran Hamra'u dama da wannan aniyar a cikin zuciyata, domin na jima ina son yarinyar itama tana sona, ba tun yau ba yarinyar take dawainiya dani, ta sadaukar da rayuwarta kaf a kaina, sannan kuma tayi min hallacin da ba zan ta'ba mantawa dashi ba, mutukar na cika dan halak dole na saka mata da alkairi, auranta kad'ai shine sakayyar da ya cancanta nayi mata, saboda haka Kawu kayi hakuri da wannan abu da ya faru hakika banji dadi ba kuma zanyi wa tufkar hanci insha Allah abu makamancin wannan ba zai sake faruwa ba."

Kawu Ado yace." To Alhamdulillhi naji dadin wannan magana, kuma nayi farin ciki daka mutuntani tare da sauran 'yan uwanka, haka ya kamata d'a na halak ya kasance duk rintsi kada ya k'yamaci asali da tushen sa domin duk abun da ya zama a duniya bai isa ya canzawa towo suna ba, saboda haka wannan kalaman naka sun faranta min rai mutuka da gaske, Allah yayi maka albarka ya kuma kare ka daga sharrin masu sharri."

Ya amsa tare da jin dadin irin adduoin da yake masa.

Gabad'ayansu har Uwalen ya tattarasu suka nufi sashen Gimbiyar, da yawa daga cikinsu hakan be musu dadi ba, saboda tsira da mutuncinsu, koda suke 'yan kauye ai mutane ne kamar kowa me zai sanya a dinga k'yamatar su har idan suka zo guri a dinga toshe hanci, wannan shine abinda yafi 'bata musu rai.

Suka cika falon taf don wasu ma a tsaitsaye suka tsaya saboda babu gurin zama, ya kallesu da

fadin." Ku dan saurari fitowa ta yanzu." suka hada baki gurin amsawa.

Koda ya shiga dakin bacci ya same ta tana yi ga airpix a cikin kunnanta wayar kuma na saman kirjinta.....'Karamar riga ce a jikinta mai karamin hannu gabadaya jikinta a waje mussaman cinyoyinta, tsigar jikinsa tana tashi ya 'karasa kusa da ita, ya daidai ta nutsuwarsa, kafin ya fara kiran sunanta.

Shuru bata motsa ba bacci take sosai.

Yasa hannu ya cire airpix din kafin ya bude muryarsa da kiran sunanta.....*"ZINATU."*

Bata motsa ba ballanatana ta san shigowarsa dakin.

Ya zauna kusa da ita yana jan kafarta.....Ya jima yana jijjigata kafin ta bude ido da mayen bacci a tare da ita take ganinsa dishi-dishi, ya sake jan kafarta da fadin." Ki tashi wane irin bacci ne haka saboda rashin hankali kuma kin sanya airpix a kunne kina bacci dashi.

Ta bude idonta sosai tare da kokarin tashi.

Kawar da kanshi yayi sakamakon hango pant d'in ta, rigar da ita gwara babu domin abunda ta rufe kad'an ne a jikinta.

Tashi tai ta kama hanyar toilet sassan jikinta na wani irin rawa sakamakon rashin sutturar arziki da babu a jikinta.

Ajiyar zuciya ya sauke bayan shigar ta toilet din ya cigaba da dabarar danne k'ulafucinsa.

Jin shuru bata fito ba ya tabbar masa da wanka take, tsaki yaja ya tsaya kofar toilet din da fadin. " Malama kiyi ki fito akwai jama'ar da suke jiran ki.

Jin abinda yace yasa ta kudiri aniyar 'bata masa rai domin dai ta riga ta san jama'ar basu wuce mutanan k'auye 'yan uwansa masu wari da hamami!

Koda ta gama wankan kin fitowa tayi tai zamanta a toilet din tana saka wasikar jaki, tayi hakan ne domin ta bata masa rai bayan haka kuma tana gujewa kanta sha'kar wari! wanda ka iya janyo mata tashin zuciya.

Buga kofar yay da karfin gaske! ya bude murya da fadin." Ke! wai ba zaki fito ba ne."'?

Tsaki! taja ta mike tana zumbura baki da gunguni ta bude kofar, suka hada ido, ganin yanda idonsa yayi jawur yasa gabanta fad'uwa, tai saurin ra'be shi ta wuce tana jin shakkar sa a

zuciyarta.

Ya bita da wani irin kallo kafin ya girgiza kanshi ya bita har dressing mirror din da take zaune.

Tana shafa mai tana sauraran maganganunshi.

"Duk irin rashin mutuncin da ki kayi wa 'yan uwana na samu labari! ki saurareni da kyau! domin ki kiyaye abunda kan iya kawo rashin jituwa a tsakaninmu, zan iya hakuri da duk abunda za kiyi amma ba zan iya kawar da kaina gurin ganin kinci zarafin iyaye da kakanni na ba, bani da kowa sama dasu, domin su sukayi min duk wani gata har na girma na kai munzali, wallahi na rantse miki da Allah akan su, babu abunda ba zan aikata ba, saboda ni na san kima da mutuncin iyayena, mutukar kina so mu zauna lafiya to dole ki mutunta min su ki kuma darajasu."

Ko gezau! duk maganganusa ba su isa su hana ta fadin gaskiya ba, ta kalleshi da fadin." Ina so a fada min abunda nai musu wanda ya sanya ka zuwa ka tsaya a kaina kana kalubalanta ai na dauka sai mutum yay laifi za'a tuhumeshi."?

Yaga kamar ta raina masa hankali da jan ido yace." Zaki 'karyata maganarsu ne? wanda ya tabbatar min da abinda ki ka 'aikata ba zai miki 'kaharu ba idan yayi miki k'arya yayi wa? ki kiyaye nifa."? jikinsa na tsuma! ya ke maganar.

Man shafawa ta dan lakato tana mutsikawa a hannuwanta kafin tace." Sai kaje ka tambayi shi wanda ya fada maka cewa naci mutuncinsu idan sharri nai musu, mai zai sanya su shigo in da nake suna wari! da tsamin hammata."!!

Hankalinta kwance take maganar domin bata tsammanin cewa hukuncin mai tsauri zai bi ta kanta ba.....Wani bahagon mari yayi mata da bayan hannunsa, wanda ya sanya ji da ganinta daukewa na wucin gadi.

Kai ta sunkuyar kasa tana mamakin al'amarin! ita ya Mara akan wasu gigidadawa!! wani katon bakin ciki yazo ya tsaya mata a wuya.

Yana tsaya a kanta yana surfa mata bala'i tare da jajjada mata muhimmacin mutanan da take rainawa har tana fadin duk maganar da ta ga dama a kansu.

Ta danne kukan da yake kokarin kufce mata tace." Ko zaka ce 'karya nake sai na fadi gaskiya domin kai kanka wari kake ballanatana su, na fad'a din."

Hannu yasa ya gwa'be bakin! zafi ya hanata karasa maganar dake bakinta.....Ido ta zuba

masa ganin yanda fatar goshinsa duk ta tattare sai wani irin gumi yake kamar ba sanyi safiya ba.

Yanda yake rawar jiki yana kai kawo a kanta yasa ta tsorata, babu yanda ta iya haka ta shirya jikinta, ya nuna mata hanyar fita da hannunsa, ba tace komai ba tayi gaba zuciyarta na wani irin zafi! tsaki mai tsayi yaja kafin yabi bayanta.

ZINATU ba tayi musu 'karya ba da gaske take tsami da wari suke shima ya san haka ya kuma ji warin a hancinsa amma saboda rashin gaskiya ya take.

Rashin gurin zama yasa taja ta tsaya a bakin kofa, ta daure zuciyarta da fadin." Ina kwananku."?

Wasu daga ciki sun amsa wasu kuma sukayi mata kallon uku saura kwata *Yo a fad'awa mutumin k'auye iyashege😅*

Bata damu da hakan domin ba sune a gabanta ba burinta taje ta amayar da aman da yake taso mata.

Jinsa kawai take yana mata bayaninsu da nuna mata muhimmanci su a tare dashi, yawu ya cika mata baki, duk ta rasa yanda za tayi, itama a karan kanta bata san abinda take sai dai don ba yanda za tayi ne.

Duk irin dauke kan da take yana lure da ita, ransa idan yay dubu ya baci! ya daure ya cigaba da cewa.

" Kada kiyi tunanin don kin fito daga gidan sarauta kinfi wasu kima da daraja! to ina so ki san cewa babu wanda yafi wani a wannan duniyar face wanda yafi bautawa Allah, duk daya muke a gurinsa, kuma shi yayi na burni yayi na kauye, kana kuma shi yayi mai kudi yayi talaka, yayi sarki yayi bafade, mulki talauci arziki duk shi yake bayarwa ga wanda yaso, saboda haka ni 'yan uwana sun fi min komai a duniyar nan don haka ba zan lamunci kici zarafinsu ba, ina so ki rike wannan, ki zauna a matsayinki na matata, suma su zauna a matsayinsu na jinina wannan shine abinda nake so ki rike kuma kiyi aiki dashi."

Uffan bata iya cewa ba to yaushe ma ta samu sararin maganar bakinta cike da yawu.

Tana kallonsu suka tashi daya bayan daya suka dinga fita, falon ya rage su biyu, harararsa tayi kafin ta bude daki ta shige kai tsaye toilet ta nufa ta zubar da yawun bakinta, tsugunawa tayi

zuciyarta na cigaba da hantsilawa.....Dole dai sai da tayi aman sannan ta samu sassauci.

Tana fitowa ta samu Baraka tana gyara dakin

Kan Sofa ta kwanta tana mayar da numfashi tace." Baraka don Allah kiyi kokari a falon nan wannan wari duk ya fice kinji ko."

Tace." To ranki ya dade insha Allah bari na gama gyara miki dakin."

Kai ta girgiza kafin ta rufe idonta tana kukan zucci! wai dangin mijin da take aure sune kucakai masu warin daud'a daddawa da tsamin hammata! wannan al'amari yana daure mata kai, a mafarki ba ta'ba tsammanin cewa za ta auri d'an 'kauye ba.

Hamra'u a ranar da al'amarin ya faru kamar ta zuba ruwa a kasa tasha saboda farin ciki taji dadin yanda ya nuna mata muhimmancinsu bayan haka kuma tayi farin ciki sosai da maganarsu ta karshe da Kawu Ado, domin kafin su tafi sai da ya jaddada mata cewa ta kwantar da hankalinta UMARU zai aureta da ikon Ubangiji, wannan shine abinda sanya farin cikinta kara nununkuwa.

Sosai ta dauki fushi dashi saboda abunda yay mata yayi masifar 'bata mata rai, da farko tayi tunanin zama dashi saboda salon soyayyarsa amma yanda yake kambaba darajar 'yan uwansa yasa duk taji ya fice daga zuciyarta, tunaninta ya za'ayi ta samu namiji wanda yay daidai da rayuwata wanda kuma ya iya love irin nashi.

